# Bayanin Umarnin INGO na 1

bond

# Yadda ake Aiwatar da Kiyayewar FCDO Daga Cin Zarafi na Jima'i, Cin Mutunci da Tsangwama (SEAH) Jagorancin Himma da ake Buƙata a Ƙungiyoyin Ƙasashen Duniya.

## Mayar da hankali kan Aukuwa: Hanyar Kariyar da Korafe-korafe da Faɗakarwa - Himma da ake Buƙata na FCDO.

Wannan shine farkon cikin aukuwa guda uku waɗanda ke nuna yadda ake amfani tukuru da 'Kiyayewa Daga Cin Zarafi na Jima'i, Cin Mutunci da Tsangwama (SEAH) Jagorancin Himma da ake Buƙata ga abokan hulɗan FCDO masu aiwatarwa' a cikin ƙungiyoyi. Wadannan nazarin aukuwa na bada misalai dalla-dalla kuma kai-tsaye na yadda aka yi amfani da jagorar a cikin kungiyoyi da aikace-aikace tare da bangarori shida na yadda za a tunkari SEAH, kamar yadda aka kwatanta a hoto na 1.




### Hoto na 1: Taƙaitawar yanki shida na himma da ake buƙata na SEAH[1]



| **Hanya ta SEAH** | **Korafe-korafe da Faɗa karwa** | **Daukar Ma'aikata da horarwa** | **Gudanarwar haɗari** | **Ka'idar aiki** | **Gudanarwa & hisabi** |
|---|---|---|---|---|---|
| Manufa | Manufa | Bayanin Aiki da Haɗari | Rukunin Haɗari na SEAH | Ka'idar aiki | Hukumar da aka Nada |
| Ma'aunai | Horo | Zaɓi da Hira | Bita na Yau-da-Kullum | Ka'idoji Shida na IASC | Mai Jagorancin Kiyayewa |
| Yara da Matasa Masu Rauni | Korafe-korafe na Ciki | Nassoshi da Bincikewa | Tara Kudaɗe | Ma'aikata Sa Hannu | Gudanarwar hukuma ta SEAH |
| Shigarwa da Masu Amfanuwa | Korafe-korafe na Waje | Gabatarwa da Horon Tunatarwa | Haɗarori na Kan-layi | | Wuraren Sa-ido na Gida |
| Agajin Wanda ya Tsira | Rijistar Aukuwa | | Abokan Hulɗa na Kasa | | Bukatar wasu |

1. Ofishin Harkokin Waje, Tattalin Arziki da Cigaba na Burtaniya(2022), Taƙaitawar yanki shida na himma da ake buƙata na SEAH. Akwai a: https://assets.publishing.service.gov.uk/government/uploads/system/uploads/image_data/file/143790/Summary-6-areas-SEAH-due-dilligence.png accessed 18 May 2022].

**Bayanin Umarnin INGO na 1:** Yadda ake Aiwatar da Kiyayewar FCDO Daga Cin Zarafi na Jima'i, Cin Mutunci da Tsangwama (SEAH) Jagorancin Himma da ake Buƙata a Ƙungiyoyin Ƙasashen Duniya.




## Yanayi

Ƙungiya mai gina zaman lafiya da ke Birtaniya abokiyar aiwatarwar FCDO ce, wacce ke karɓar kuɗaɗe £1.2m a cikin shekaru 3 don gabatar da bita da gudanar da bincike ta hanyar masu ba da shawara. Suna aiki tare da haɗin gwiwar ƙungiyoyin gida guda biyu, waɗanda su ne abokan hulɗa na ƙasa. Aikin ya ƙunshi taron tattaunawa don tattaunawa kan yadda ƙungiyoyin matasa masu shekaru 16 zuwa 25 za su iya shiga cikin ayyukan zaman lafiya a tsakanin al'umma. Har ila yau, ya ƙunshi tattara bayanai, waɗanda masu tattara bayanan gida suka yi, game da ɗanɗanawar matasa a lokacin rikici a CAR, Fakistan da Filipains don rahoto. Kashi 40% na wannan tallafin yana zuwa ga waɗannan ƙungiyoyin gida kuma ɗaya daga cikin waɗannan ƙungiyoyi na aika kuɗi zuwa wata ƙaramar ƙungiyar.

Misalan da aka zayyana a ƙasa sune mafi kyawun buri kuma ana iya daidaita su dangane da haɗarin gaba-ɗaya don tabbatar da cewa an yi la'akari da daidaito.

A ƙasa akwai tambayoyi masu nuni da FCDO game da hanyar kiyayewa da korafe-korafe da fadakarwa da Gudanarwa da Hisabi waɗanda ake amfani da su yayin kimantawar kima FCDO na ƙungiyoyin abokan hulɗa. INGO na nuni ga waɗannan tambayoyin yayin gudanar da himma da ake buƙata na abokan hulɗarsu don tabbatar da cewar an dasa amintattun matakan kiyayewa na SEAH da suka dace kuma ana bin ka'idoji.

## Hanyar Kiyayewa

- Shin akwai wata manufa ta kiyayewa, kuma ta shafi musamman cin zarafi na jima'i da cin mutunci da tsangawa na jima'i? Idan ba haka ba, kuma akwai aiki da yara, matasa ko manya-dake-cikin-haɗari to dole ne a sami takamaiman manufofin da suka shafi waɗannan rukunoni kuma dole waɗannan su magance haɗarin SEAH. Idan babu wata manufa ta kiyayewa ko aiki da waɗannan rukunonin, dole ne a sami manufofin cin zarafi na jima'i da tsangwama da cin mutunci waɗanda ko dai su kaɗai ke tsayuwa ko kuma wani bangare ne na babban littafin-hannu na HR.
- Shin manufar ta ƙunshi bayanin alƙawarin ku na kiyayewa, kamar bayanin rashin uzuri ga tunkarar tsangwama na jima'i da cin zarafi na jima'i da cin mutunci kuma da rashin daukar matakin rashin ba da rahotonsu?
- Shin ana sanar da ma'aikata da masu cin gajiyar shirin game da ƙudurin ƙungiyar don kiyayewa da kuma yadda za su iya gabatar da korafe-korafe ko damuwa? Ra'ayoyin masu cin gajiyar suna tasiri a kira da aiki na hanyoyin bayar da rahoto
- Shin ƙungiyar ta bayyana yadda za ta ba da tallafi ga wanda ya tsira ko wanda aka azabtar da SEAH ta daya daga ma'aikatanta ko abokin aiwatarwarta? Shin ta yi tunanin ta hanyar wanda zata iya ba da rahoto ga aukuwar gareshi da abin da take buƙatar la'akari don tabbatar da tsarinda ke kula da wanda ya tsira?
- Shin ƙungiyar ta fayyace waɗanne hukumomi ne take bukactar kai masu rahoton lamarran SEAH a kasar da take gudanar da ayyukanta? Kuma ta yi la'akari da yanayin da irin wannan rahoto ba zai iya zama da tsari ga waɗanda suka shafu ba?
- Shin akwai wani tabbaci mai zaman kansa na riko da abubuwan SEAH na Ainihin Ka'idar Bil-Adama, misali ta hanyar HQAI, ko Mafi Kaƙancin Ka'idojin IASC akan PSEA?

## Korafe-korafe da faɗakarwa

- Shin ƙungiyar tana da bayyanannniyar tsarin da ke ba da damar ta da korafe-korafe ko damuwa daga waje da cikin ƙungiyar, kuma an horar da ma'aikatan yadda za su gudanar da shi?
- Shin akwai wata manufa ta fadakarwa wacce ke ba da kariya ga masu fadakarwa daga ramuwar gayya kuma ta ƙunshi bayyanannun matakai don magance matsalolin da aka tayar kuma ta waye da kuma lokutanda aka yi?
- Shin ƙungiyar tana daukar cikakken rajista na kariyar zarge-zargen da aka tayar da kuma yadda aka magance su?
- Shin hanyoyin korafe-korafen suna akan waɗanda suka masu tsira kuma an tsara su don tabbatar da sirri da kuma guje wa sake gallazawa?



## Menene tsarin himma da ake bukata na FCDO yayi kama?

**FCDO tana aiwatar da kididdigar ƙimar himma da ake buƙata akan abokan hulɗa kafin shigan cikin yarjeniyoyin tallafin kuɗi da su.**

⇩

**Abokin aiwatar na aiwatar da himma da ake buƙata akan abokan hulɗa na ƙasa kafin shiga cikin yarjeniyoyin tallafin kuɗi da su, ko dai ta hanyar bitar tebur, zuwa wurin aiki, tsararrun tambayoyin, tambayoyin kai-tsaye ko taron bita ko gaurayarsu.**

⇩

**FCDO na iya neman shaida cewa an yi warwarar manufofin kiyayewa na SEAH ta abokin aiwatarwa zuwa kasan sarkar isarwa.**


## Yadda aka aiwatar da jagorancin kiyayewar himma da ake bukata na FCDO ta ƙungiyar gina zaman lafiya zuwa ga abokan hulɗarta na ƙasa.

Kafin sanya hannu kan Yarjejeniyar Haɗin gwiwa, abokin aiwatarwar na gudanar da kimantawar ƙima na himma da ake buƙata da abokan hulɗa na ƙasa, don fahimtar menene takamaiman haɗarin kiyayewa na shirin, da kuma kafa yadda manufofi da tsare-tsare na kiyayewa ke magance haɗuran. Abokin aiwatarwar zai yi amfani da bayanan da aka tattara don gano idan isassun tabbaci na a ƙafe don cigaba da ba da tallafin kuɗin ko a'a.

## Manufar kiyayewa

Kungiyar abokin hulɗa na ƙasa mai yiwuwa ba ta da manufar kiyayewa; duk da haka, za su iya yin rajista don aiwatar da manufofin abokan hulɗa (tabbatar da an rabar da shi da fahimtarsa ga duka ma'aikatan da suka dace) da nufin haɓaka nasu a ƙarshen aikin, ta amfani da tsarin aiki. Hakanan ya kamata ƙungiyoyin abokan hulɗa su yarda su yi amfani da tsarin aiki don wasu wuraren rauni

Abokin aiwatarwa na yin rikodin abokin hulɗa na ƙasa da bashi da wata manufa ba a matsayin haɗari mai saura kuma yana goyan bayan shirin aiki don abokin aiwatarwa na ƙasa don gina manufofi a ƙarshen shirin, yayin da yake bayyanawa ga duka wanda ke da hannu cewa abokin aiwatarwa na ƙasa yana daure da manufofin abokin aiki mai aiwatarwa da suka dace a wannan lokacin. Ana iya yin rikodi a kuma haɗa matakai don rage haɗari da haɓaka ƙwarewar abokin aiki a matsayin wani ɓangare na tsarin kula da haɗari na ayyukan alheri masu gudana.



## Yara da Matasa da ke fuskantar Haɗari

Fahimtar abokan haɗin gwiwa game da mahallin gida don GBV/SEAH game da dokokin ƙasa da ƙa'idodin zamantakewa na gida waɗanda ke taimakawa ko hana mu'amala da SEAH sun sanar da hanyoyin kiyayewan. Bisa ga wannan fahimtar, abokan hulɗa na ƙasa suna ba wa ma'aikatan su da masu ba da shawara na dogon lokaci manufofin kiyayewa, wanda sun shafi SEAH, don tabbatar da cewa suna kula da hanyar da za ta dace don hulɗa da waɗanda suka fito daga al'ummomin da ake wa wariya, yara, matasa, da manya da ke cikin haɗari.


Manufofin sun haɗa da sanarwar kudurin kiyayewa da kuma nuna rashin uzuri ga SEAH.

Abokin aiwatarwar yana sane da cewa akwai sauran haɗarin da ya rage a kewaye da rashin samun dawowar bayanan binciken duba laifuka. An bayyana wannan a cikin tsarin tafiyar da haɗarinsu don shirin.

## Ma'aunai

Abokan hulɗa na ƙasan suna ba wa ma'aikata da masu ba da shawara ƙa'idar aiki wanda musamman ke hana SEAH, yana nuna ƙa'idoji shida na IASC akan PSEA da kuma bayyana sakamakon laifuffuka, don tabbatar da cewa ma'aikata da masu ba da shawara suna sane da alhakin su na tafiyar da mutane cikin tsari lokacin da suke. tuntuɓar masu ruwa da tsaki. Ma'aikatan suna sane da kudurin ƙungiyar don kiyayewa ta wurin waɗannan takaddun. Ma'aikata suna samun horo akan waɗannan manufofin kowace shekara.

Abokin aiwatarwar ya fahimci ragowar haɗarin cewa ko da yake ana ba da horo kan manufofin kowace shekara, har yanzu ana iya samun keta manufofi. Ana rage wannan ta hanyar aiwatar da tsarin ladabtarwa a yayin da aka yi mummunar ketawa na waɗannan manufofin.



A dunkule, abokan aiwatarwa da abokan hulɗa na ƙasa su tsara tsarin kukan al'umma, ta yadda shugaban al'umma ke taka rawa wajen sasantawa don warware koke-koke.

Abokan hulɗa na ƙasa su bayyana wa mahalarta waɗanda ke amfani da sabis na ƙungiyoyi, a cikin yare na yankin da kuma ta hanyoyin sadarwa iri-iri, a farkon ayyukan game da haƙƙin zama cikin tsari, gami da daga cin zarafi na jima'i, cin mutunci da tsangwama, wariya da shirye-shirye marasa aminci, misali, sufuri da masauki mara aminci. Ana ƙarfafa mahalarta su ba da ra'ayi game da batutuwan tsaro iri-iri, ba kawai SEAH ba, don daidaita hanyoyin amsawa da nuna hisabin ƙungiyoyi gare su.

Abokin aiwatarwar ya fahimci cewa mahalarta ba za su sami ikon sadar da ra'ayi ba saboda rashin daidaituwar ikon da ba a gani wanda aka gano a matsayin ragowar haɗari kuma ana rage shi ta hanyar samun hanyoyin sadar da ra'ayi iri-iri don cigaba da sa ido ta hanyar abokin hulɗa na ƙasa.

## Tsarin korafe-korafe na ciki

Abokan hulɗa na ƙasa suna bayyana a farkon ayyukan cewa, idan mahalarta suna da damuwa / jin rashin tsaro saboda ayyuka ko halayen ma'aikata ko sauran mahalartan, za su iya magana da kowane mai gudanarwa yayin aiki. Suna da fastoci sama a wurin aikin da ke bayanin cewa zaku iya magana da kowane mai gudanarwa a mutum-da-mutum da kuma ta lambar waya don ƙungiyar abokin aiwatarwa. A cikin bitar himma da ake buƙata, abokin aiwatarwar yana ba da shawarar cewa abokan hulɗa na ƙasa su haɓaka zaɓin rahoton mara-nuni, kamar imel ko akwatin ra'ayi kuma wannan ya zama wani bangare na shirin aikinsu.

Abokan hulɗa na ƙasa suna da fastoci masu bayanin cewa mahalarta zasu iya ba da rahoto ga abokin aiwatarwa game da ƙungiyoyin su idan wani memba na al'umma ya sami rauni ba da gangan ba saboda aikin ƙungiyar ku kuma bai so ya ba da wannan bayani ga ƙungiyar ku kai-tsaye ba.

Abokin da ke ƙasa da abokin aiwatarwa su fahimci cewa akwai ragowar haɗarin cewa yin rahoto ga abokin aiwatarwa na iya zama da ƙatsewa, ganin cewa abokin aiwatarwar ba ya a cikin mahallin yankin kuma ya rage wannan ta hanyar tabbatar da cewa abokan hulɗa na ƙasa sun shirya don karɓar rahotanni, kiyaye bincike akai-akai na zabuɓɓukan bayar da rahotanni mara-nuni na gida da neman jagora daga abokai masu aiwatar lokacin da aka sami damuwa.

## Korafe-korafe na waje da bada rahoto ga hukumomi

A cikin kididdigar ƙimar himma da ake buƙata, abokan hulɗa na ƙasa suna ambaton hanyoyin korafe-korafe na ciki da na waje da aka samar. Waɗannan an sanar da su ta hanyar ra'ayi na al'umma kuma suna da takamaiman mahalli don tabbatar da cewa al'umma sun amince da su da kuma tsarin da masu amfani ke ganin halal ne. Bayan sanar da mahalarta yadda ake ba da rahoton abubuwan da suka faru, abokin aiwatarwar zai saurari duk wata damuwa da mutumin da ke jin rashin tsaro ya taso yayin wani aiki, su gano duk wani haɗari na gaggawa a gare su.

A inda yake da aminci a kai rahoto ga 'yan sanda, ana iya buƙatar binciken 'yan sanda ƙafin tsarin ƙungiya wanda hakan ke nufin za a iya dakatar da tsarin ƙungiyar a wannan lokacin. Ya kamata abokin hulɗa na ƙasa ya yi la'akari da bayar da rahoton abubuwa muhimmai ga shugaban al'umma sai dai idan yin hakan zai kawo damuwa. Rashin yin hakan na iya nufin babu wani kuduri a hangar al'ummar. Hakanan zai iya jefa ma'aikatan abokin hulɗa na ƙasa cikin haɗari idan ba a gansu suna bin matakin da ya dace na al'umma ba.

Abokin hulɗa na ƙasa zai kididdige ƙimar ko an sami wani sabawa manufa, bayar da rahoto ga abokan aiwatarwa idan haka ne da takaitaccen rahoton, gano haɗarin da kuma gabatar da matakai na gaba. Abokin aiwatarwar zai shigar da wannan bayanin kuma ya watsa shi cikin gida zuwa manyan masu gudanarwa da amintattu - za su sadar da wannan bayanin ga FCDO daidai da kalmomin da ke cikin yarjejeniyar tallafin kuɗin. Idan abokin aiwatarwar yana da rajista a Ingila da Wales, ana buƙatar a kai rahoto ga manyan al'amura (ciki har da kiyayewa) zuwa Hukumar Ba da agaji ta Ingila da Wales (CCEW). Idan babu wani babban laifi, za su yi la'akari da yadda za su tallafa wa wanda ya tsira kuma su yi amfani da darasi daga wannan a nan gaba.

Abokin aiwatarwar yana sane da cewa kai rahoto ga 'yan sanda a matakin yanki yana fuskantar haɗari ga mutane daban-daban da suka shafu kuma rashin ba da rahoto ga hukumomin gida ragowar haɗari ne - ana rage wannan ta hanyar tabbatar da cikakken bincike da bayar da rahoto ga FCDO da CCEW, gudanar da kimantawar ƙimar haɗarin yayin da ake gudanar da bincike don rage maimaita laifuka.

**Bayanin Umarnin INGO na 1:** Yadda ake Aiwatar da Kiyayewar FCDO Daga Cin Zarafi na Jima'i, Cin Mutunci da Tsangwama (SEAH) Jagorancin Himma da ake Buƙata a Ƙungiyoyin Ƙasashen Duniya.

## Korafe-korafe da faɗakarwa

Abokin hulɗa na ƙasa zai bi tsarin bincike kuma ya cigaba da ciyar da abokin aiwatarwar sabuntawar abubuwa. Ana iya dakatar da ma'aikacin yayin wannan bincike idan yin hakan ya fi aminci. Idan binciken ya tabbatar da an yi babban kuskure, za a dauki mataki daidai da manufa da ladabtarwa. Abokin hulɗa na ƙasa yana riƙe da bayanin duka zarge-zargen kiyayyewa/bayanan da aka ba da rahoto da yadda aka sarrafa su.

A matsayin wani ɓangare na kimantawar ƙima himma da ake buƙata, masu aiwatarwa da abokan hulɗa na ƙasa suna da shaidar cewa duk suna da manufa ta fadakarwa, wacce ke samuwa ga kowa da kowa kuma tana aiki (an tabbatar da aikin ta hanyar neman shawarwarin doka don tabbatar da kariya na samuwa a yankin).

Yakamata abokan aiwatarwa da abokan hulɗa na ƙasa su yarda da matakai don gudanar da bincike na haɗin gwiwa da gudanar da shari'o'i, don ƙarfafa abokin hulɗa na ƙasa da kuma neman tabbaci don abokin aiwatarwar.

Abokin aiwatarwar ya fahimci cewa gibi bayanan ragowar haɗari ne kuma zai iya ba da damar sake yin laifi - don rage wannan, ƙungiyoyin biyu su zama a bayyane da bayanan da aka karɓa da juna.

## Agajin wanda ya tsira

Jagoran sadaukarwa don kiyayewa a cikin ƙungiyoyin abokin hulɗa na ƙasa na iya tallafawa masu gudanarwa da bayyanawa, bayan ya yi horon kan layi game da karbar bayyanawa da binciken SEAH.

Abokin aiwatarwa da abokin hulɗa na ƙasa tare su zana taswirar da ke da ayyuka na tallafi. Za a bai wa wanda ya tsiran tallafi, wanda zai iya haɗawa da na doka, likita, kwakwalwa da zamantakewa, ko tallafi na aiki. Wannan tallafin zai kiyaye sirrin wanda ya tsira kuma ya tabbatar da cewa sake gallazawa bai faru kuma ba. A lokacin tsarin himma da ake buƙata, abokin hulɗa na ƙasan ya gane cewa yawancin wannan tallafin baya samuwa a cikin mahallin. Sakamakon haka, ana iya buƙatar kawo wannan tallafin daga wani mahallin, wanda abokan aiwatarwa da abokin hulɗa na ƙasan za su nemi ganowa yayin aikin. Saboda ƙarancin kuɗi, wannan na iya yiwuwa ne kawai na ɗan gajeren lokaci fiye da idan akwai tallafi na wanda yai tsira a cikin wannan mahallin. Ana ƙarfafa abokan aikin aiwatarwa don tattaunawa game da kiyaye kashe kuɗi da FCDO.

Abokin aiwatarwa na ba da shawarar cewa ba za a iya shigar da tallafin wanda ya tsira ba saboda ƙaranci na yankin, wannan a matsayin ragowar haɗari wanda aka rage ta hanyar tabbatar da cewa an binciko duka hanyoyin tallafawa waɗanda suka tsira ciki har da ayyukan da gwamnati ke bayarwa, Majalisar Dinkin Duniya, kungiyoyi masu zaman kansu da sauransu.

## Muhimmanci abubuwan dubawa don kyakkyawan aiki da himma da ake buƙata na ƙungiyar ku.

| Manyan shawarwari... | Don la'akari da... |
|---|---|
| Ba da damar abokan hulɗa na ƙasa su yi rajista ga manufofin kungiyar masu aiwatarwa idan ba su da nasu.<br><br>Yi la'akari da cewa abokan hulɗa na ƙasa ba zasu zama da girma ko samun kayan aiki don aiwatar da wannan manufar gaba ɗaya ba kuma wani ɓangare na shi bazai aikatu a aikin su ba.<br><br>Gano sassan da ba za su iya aikatawa ba. | Tabbatar da cewa abokan hulɗa na ƙasa suna da manufofinsu ko kuma sun sanya hannu kan manufofin abokin aiwatarwa don su san ingantattun matakan bayar da rahoto.<br><br>Idan an yanke shawara don yin haɗin gwiwa da ƙungiya ba tare da manufar kiyayewa ba, don haka wajen ɗaukar abokan aiwatarwa, yakamata amintattu suyi la'akari da ɗaukar bayanin wannan shawarar, yawanci wannan wani ɓangare ne na taron amintattu na yanayin gudanarwa. FCDO na buƙatar ƙungiyoyin da ke hulɗa da yara ko manya da ke cikin yiwuwar haɗari su sami samar manufar kiyayewa a ƙasa. |
| Yawancin abokan hulɗa na ƙasa na fi kasance wadanda masu ɗaukar bayyanawa daga mahalarta da kuma gano haɗarin nan take ga mahalarta, la'akari da babban rashin daidaituwar iko da abokan aiwatarwa da ke waje da mahallin. | FCDO na buƙatar abokan hulɗa su gaggauta tuntubar su a Reporting reportingconcerns@fcdo.gov.uk don ba da rahoton duk wani zarge-zargen SEAH, inda waɗannan ko dai suna da alaƙa ta kai tsaye da yarjejeniyar ba da tallafin kuɗi ko kuma inda za su yi tasiri sosai ga haɗin gwiwar.<br><br>Hakanan ana buƙatar a ba da rahoton munanan abubuwan da suka faru ga hukumar agaji ta hanyar RSI. |

**Bayanin Umarnin INGO na 1:** Yadda ake Aiwatar da Kiyayewar FCDO Daga Cin Zarafi na Jima'i, Cin Mutunci da Tsangwama (SEAH) Jagorancin Himma da ake Buƙata a Ƙungiyoyin Ƙasashen Duniya.

Lokacin haɗin gwiwa da abokan hulɗa na ƙasa, abokin aiwatarwar zai yi la'akari da abubuwan aiki masu zuwa:

- Yadda za a tallafa wa abokan hulɗa na ƙasa don haɓaka nasu kiyayewa daga manufar SEAH
- Yadda abokan hulɗa na ƙasa za su iya haɓaka hanyar ba da rahoto mara suna
- Yadda za a shawo kan rashin kayan tallafi na wanda ya tsira a cikin mahallin cikin ma'ana kuma daidai gwargwado

Tabbatar da cewa yayin bayyanawa daga mahalarci, ana gano haɗarin nan da nan, kuma ana ba da tallafi ga mahalarci a hanyar da ta shafi wanda ya tsira.

Tabbatar da cewa matakinku na farko na yin aiki da abokan hulɗa na ƙasa baya kammala kimantawar ƙimar himma da ake buƙata. Gina dangantaka da abokan hulɗa na ƙasa zasu tabbatar da yin aiki a cikin kimantawar ƙimar himma da ake buƙata. Ƙila ba za a iya gudanar da kididdigar ƙimar himma da ake buƙata da ya dace ba ta hanyar layi ɗaya - wasu abokan hulɗa na ƙasa na iya samun wahalar kammala tambayoyin kuma suna iya fifita hanyar haɗin gwiwa da abokan aiwatarwa.

Abokan hulɗa na ƙasa na iya samun ƙarin zurfin fahimtar al'ummomin yankin. Taimakon wadanda suka tsira daga abokan hulɗa na ƙasa na iya bambanta da abokan aikin aiwatarwa. Tabbatar da cewar abokan hulɗar aiwatarwa sun haɗa da abokan hulɗa na ƙasa a cikin cigaban goyon bayan wanda ya tsira.

Tabbatar da cewa abokan hulɗa na ƙasa suna haɓaka shirin aiki da ɓangarorin da aka ba da shawarar (dogaran shirye-shirye) suna haɗe, bisa ga wuraren rauni. Ya kamata a fahimci cewa, musamman idan ba tare da ƙarin tallafin kuɗi don wannan manufa ba, zai ɗauki lokaci don aiwatar da himma da ake bukata a cikin ƙungiyoyin su. FCDO tana ƙarfafa abokan hulɗa na ƙasa don neman kuɗi don kiyayewa, inda ake buƙata.

Matsalolin harshe na iya haifar da ruɗani a manufofin da abokan hulɗa na ƙasa za su iya yin rajista.

Waɗanda ke aiki a cikin ƙungiyoyin abokin hulɗa na ƙasan ba za su iya fahimtar harshen manufar ba. Yakamata abokin aiwatarwar yayi aiki da abokan hulɗa na ƙasa don fassara manufa zuwa harshen yankin da aka fahimta da kalmomin da suka fahimta.

Yakamata abokan aiwatar su bibiyi da adana bayanan duk wani ragowar haɗarurruka, tabbatar da cewa cikakken bayani na yadda aka rage haɗarurruka ya kasance gefe-da-gefe da duka haɗarurruka. Ya kamata a yi bitar waɗannan akai-akai idan akwai canje-canje ga haɗarurrukan. Ya kamata a sanar da abokan hulɗa na ƙasa game da haɗarurrukan kuma a sanar da duk wani canje-canje na haɗarurrukan ga abokan aiwatar.

Jagorar Harshe na Bond wanda ke taƙura wa 'fitar da siyasa da mulkin mallakan Burtaniya daga harshenmu' wanda za a iya samu a nan Bond na ba da shawarar yin amfani da shi yayin gudanar da himma da ake buƙata. Duk da haka FCDO ba ta yarda da amfani da siyasar ko mulkin mallakan Biritaniya ba a bayan amfani da kalmar 'masu amfanuwa' (ko wasu kalmomi a cikin jagorarta) - FCDO ce ta yi amfani da wannan kalmar don dacewa da kalmomin da aka yi amfani da su a cikin mahimman takaddun kiyayewa na ƙasa-da-ƙasa.



**Bond ita ce hanyar sadarwar don ƙungiyoyin Burtaniya masu aiki a cigaban ƙasa-da-ƙasa. Muna haɗin kai da tallafa wa cibiyoyin sadarwa daban-daban na ƙungiyoyin jama'a fiye da 350 don taimaka wa kawar da talauci a duniya, rashin daidaito da rashin adalci. Nemo ƙari a bond.org.uk**

Bond, Society Building, 8 All Saints Street, London, UK N1 9RL
T +44(0)20 7837 8344 E info@bond.org.uk